
# TAFIYAR ƘOƘI DA GIZO DON GANIN RUWAN ƘASA...

## ZUWA SASHEN TARUWAR RUWANA ƘARƘASHIN ƘASA



Masu ƙirƙirar labari Leanne Appleby da Peter Russell
Mai zane da tsara littafi Fortunato Restagno
Mai fassara zuwa Aminu Ibrahim

© 1993 Leanne Appleby, Peter Russell (rubutu)
© 1993 Fortunato Restagno (zane)
ɗab'i na farko, Nuwamba, 1993
ɗab'i na biyu, Maris, 2017
Littafin dijital na 3, Yuli, 2020
Littafin dijital na 4, Disamba 2020
Littafin dijital na 5, Fabrairu 2021
Littafin dijital na 6, Satumba, 2021
Littafin dijital na 7, Satumba, 2021
Littafin dijital na 8, Satumba, 2021

Haƙƙin mallaka
Gidan Tarihin Kimiyar ƙasa

ISBN 978-1-7778409-0-7

Haƙƙin yaɗawa:
Gidan Tarihin Kimiyar ƙasa
University of Waterloo, Ontario, Canada N2C 3G1

Mai fassara zuwa Aminu Ibrahim

# Tafiyar ƙoƙi da gizo don ganin ruwan ƙasa...
zuwa sashin taruwar ruwan a ƙarƙashin ƙasa

Masu ƙirƙirar labari Leanne Appleby da Peter Russell
Mai zane da tsara littafi  Fortunato Restagno
Mai fassara zuwa Hausa Aminu Ibrahim

Godiya ga Deanna Arm-
strong
ta Youngstown, Alberta
don taimakawa wurin ha-
sashen yadda tana ke gane
ruwan ƙasa.



Ƙoƙi tsutsace irin tana data fito daga cikin ƙasa mai danshi goye da jakar kayan aiki a bayanta, tana cewa “kai yau fa rana ce ta musamman saboda wannan tafiya”. Yayin da hadari yake haduwa, ƙoƙi ta fara tunanin ruwa za’a yi nan da nan ta keta a guje cikin sarari.



Can saman ƙoƙi, cikin hadari gizo watau ɗigon ruwa da abokanan-sa ɗiggen ruwa Suna shirin sabuwar tafiya zuwa karkashin kasa.



Ƙoƙi ta duba sama lokacin da gizo yake shirin sauka ƙasa. Sai ko ta kai hannu ta kama shi. Sauran ɗiggen ruwan suka fantsama ƙasa suka nitse cikin kasa.



Kai ji abin mamaki gizo bai nutse ƙasa ba.




Ɗigon ruwa gizo, yace nine gizo ya zama dole inbi abokaina in nutse ƙasa ‘nutsewa’ kuma? ƙoƙi ta tambaya. gizo ya kwace daga hannun ƙoƙi yaci gaba da bayani “ idan ɗigon ruwa ya sauka ƙasa, ya nutse cikin ƙasa shi ake kira tsotsewa” ko zaki biyoni?



Ina zuwa gizo, ƙoƙi ta fiddo da shebur daga jakar ta, cikin sauri ta fara tonon kasa daga busasshiya mai laushi da sauƙ in tonawa zuwa mai ƙarfi da wahalar tonawa. ƙoƙi tace kai wannan aiki da wuya.




Ruwa ya fara cika ramin, sai ƙoƙi tace ban taba zuwa matattarar ruwan ƙasa ba" nan da nan tasa takunkumin numfashi don ta shiga duk inda gizo ya shiga.




Lokacin da ƙoƙi ke share wasu baraguzai, ta ke cewa “nan da saukin tonawa”.



“Barka da zuwa matattarar ruwa ta ƙarƙashin ƙasa ke tana,” inji gizo. Sunana ƙoƙi, to ƙoƙi “kinga nan wurin. Yanzu Muna cikin shimfidar duwatsu mai dauke da magudanan dake ruwa kewaye da ruwa.



Abokanan gizo suna ta wucewa ta tsakanin ɓaraguzai, tsakuwa da lallausan yashi, suna kutsawa da dannawa zuwa magudanai can ƙasa.



Ƙoƙi tayi ta tono da sauri sauri cikin lallausan yashi, ta na ta ƙoƙarin kasancewa da gizo duk inda ya shiga.



Ƙoƙi da gizo sun isa shimfiɗa mai rike ruwa, inda ɗiggen ruwa suka kafe ba damar wucewa. Ƙoƙi ta tambayi gizo, me suke yi anan? Gizo yace nan ne madakata, wasu diggen ruwa na ta kokarin kutsawa amma suna daɗewa sosai kafin su wuce.



Yayin da suka yi gaba, sai aka fara jansu zuwa wani bututu ta cikin ƙasa. " taimako" gizo yafara kururuwa, yana cewa mun shige cikin rijiya, ƙoƙi ta tambaye shi, rijiya kuma?



Gizo yace can a doran ƙasa ne wani ya sanya bututun karfe cikin ƙasa don jawo ruwa, shi wannan mutum sunan sa mista matin da yake cika bokiti da ruwa don shayar da aladunsa. Wasu daga cikin ɗiggen ruwan kuma suna tserewa daga bokitin don koma wa matattarar ƙarƙashin ƙasa.



Cikin kulawa suka wuce butututun rijiyar, gizo yace “ ji abokaina suna ta kutsawa daga magudanan ruwa zuwa tafkin ɗiggen ruwa” sannan ya tambayi ƙoƙi ko zata iya ninkaya, koki tace a’a, gizo yace to shikenan. Zo mu koma inda ba ruwa inda ƙawayenki ke rayuwa.



Koƙi ta cire takunkumin numfashi, tace, kai! iska mai daɗi, Ruwan sama ya dauke.



Sun sauka kan duwatsu masu laima. Koƙi ta tambayi gizo "tsawon wane lokaci tafiyar nan ta dauke mu? Gizo yace " bawani lokacine mai tsayiba", "inda mun tafi dai dai da abokaina da ya daukemu satika zuwa shekaru kafin mu iso nan".



Gizo nan da nan ya fara ɗaukar ɗumi, ya daina jin nauyin jikinsa ya fara kururuwa “ wayyo ina zagwanyewa. Koƙi tace karka damu wannan shirin  wata tafiyar ne ba da daɗewa ba, sai mun hadu.



Gizo ya zagwanye kamar yadda ruwa yake zama tururi nan da nan yayi sama  cikin girgije, ƙoƙi tace “na gode” na gode da wannan gagarumar tafiya, ka dawo da wuri fa.



Bayan gizo ya gama zagwanyewa, ƙoƙi tai ta tunanin yadda tafiyarsu ta kasance a zuciyarta. Yanzu ta san yadda ruwa yake zagawa tsakanin sama da ƙasa, kuma ta tabbata zata sake haduwa da gizo.

# Kundin ma'ana

**Gumi**
Ruwan da tsirrai da dabbobi ke amfani dashi yana tashi ya bi iska a matsayin tururi. zaka iya ganin ruwan da kake fitarwa ta numfashinka a lokacin sanyi ko akan gilashi in kayi numfashi akai.

**Kewayen ruwa**
Ruwa na kewayawa ne tsakanin sararin sama zuwa ƙarƙashin ƙasa. Ruwa na zubowa ƙasa yayin ruwan sama ko narkewar ƙanƙara, sannan ya bi iska zuwa sama idan ruwan ya canja zuwa tururi daga ƙasa, da koguna, ƙoramu, da tekuna da sauransu.

**Ma'ajiyar ruwa**
Inda ruwa yake taruwa a ƙarƙashin ƙasa da za'a tarar in an tona rijiya. Duk idon ruwa suna saman ma'ajiyar ruwa.

**Madakata**
Shimfiɗar duwatsu, yashi mai  laushi ko laka mai hana gudanar ruwa zuwa ga rijiyoyi. Ruwa yana wucewa kaɗan kaɗan a wannan sashe na mariƙar ruwa.

**Magudana**
Sashin ƙarƙashin ƙasa mai duwatsu da kasa dake ƙunshe da ruwa isasshe zuwa rijiyoyi, ruwa mai gudana a ƙasa.

## Matattara
Sashin taruwar ruwa a ƙarƙashin idon ruwa inda duk wasu kafofi tsakanin dutse, ɓamɓori, ɓaraguzai, da yashi ke cike da ruwa.

## Rijiya
Wannan shine ramin da ake tonawa ko haƙawa don zuƙo ruwa daga magudana. Kamar wani bututune acikin ƙasa.

## Sashen wucewa
Ɓamɓori, ƙasa da laka ko duwatsu a ƙarƙashin ƙasa inda kafofi da saƙo ke cika da ruwa da iska don wucewar ruwa zuwa ma’ajiya.

Ruwan dake wucewa ƙasa ta wannan sashe yana jawo ma’ajiyar ruwa ta kusanci doron ƙasa bayan ruwan sama ko narkewar ƙan ƙara, a lokacin rani ma’ajiyar ruwa na ƙara yin ƙasa.


## Tsotsewa
Wannan shine yadda ruwa ke nutsewa ta kafofin ƙasa, ɓamɓori da duwatsu.

**Tururin ruwa**
Tururin ruwa ne ke bin iska zuwa sararin sama, ya narke ya zama hadari don cigaba da kewayen ruwa.

**Zagwanyewa**
Chanjawar ruwa zuwa tururin iska yana farawa ne a doran ƙasa inda ƙasa ke bushewa bayan ruwan sama.

Wallafar Gidan tarihin kimiyar ƙasa, Jamiar Waterloo, Sashen binciken ruwan ƙasa na Waterloo, da kuma Kamfanin Edviro, Waterloo, Ontario, Canada. ©1993.

Masu ƙirƙirar labari Leanne Appleby da Peter Russell, mai zane Fortunato Restagno, mai fassara zuwa Hausa Aminu Ibrahim.



FORTUNATO RESTAGNO © Oct. 1992

EARTH SCIENCES
museum
UNIVERSITY OF WATERLOO

https://uwaterloo.ca/earth-sciences-museum/

An buga a Canada

Daga Canada